

Gata nan gata nan ku.

Akwai wani gari mai suna Tola.

A garin an yi wani mai rowa.

Ba shi da aboki don tsananin rowa.



Sarkin rowa ba ya yin alheri.

Ba ya taimakon kowa.

Babu ruwan kowa da shi dan rowa.




Sarkin rowa ya koma jeji

shi kaɗai.

Jejin ya na da birai da

yawa.



Sarkin Rowa na yi wa

kansa rowa.

Ba ya cin abibcin.

Ba ya son abinci ya kare.

Yunwa ta addabe shi

saboda rowa.




Sarkin rowa ya ɓoye abinci.

Birai sun gan abincin.

Sun ci sun yi kiɓa.

Sarkin rowa ya rame.



Sarkin rowa ya kamu da ciwo.

Mutane sun hakura da rowan shi.

Cikinsa bata hakura ba.



Birai sun ji tausayin

sarkin rowa.

Suna ta bashi ayaba.



Birai sun koya wa sarkin

rowa darasi.

Ya daina rowa.

Ya koma cikin jama'a.